# Addini Ba Tikitin Shiga Sama Bane



Wani mutum, wanda ba zato ba tsammani, rashin lafiya ta katse masa hanzari na kwazon sa cikin harkokin rayuwa da kasuwanci da kuma muhimmin matsayi a Ikilisiya wadda ake darajanta shi, ya sami zarafin yin tunani. Da, lokacin yana cikin koshin lafiya kuma yana bada kokari a cikin hidimomin addini, ba ya taba tsayawa ya gwada matsayinsa a gaban Allah ba, balle har ya yi tunanin inda za ya je bayan ya gama rayuwarsa ta wannan duniya.

Wata rana, wani abokinsa ya zo gaishe shi. A cikin hirasa sai wannan aboki ya ce da wannan dankasuwa mara lafiya, “Na taba zuwa bakin mutuwa sau da yawa, kuma ba na iya bayyana irin salama da dadin da ni kan ji a duk lokacin da na ga kamar ina gaba da saduwa da Allah, domin ina dogara ga jini mai tamani na Yesu Kristi a matsayin tikiti ko izini na kadai na zuwa gaban Allah.”

Sai mara lafiyar ya daga kai ya ce, “Yan kwanakin nan ina tunani sosai akan wannan magana. Ina jin kamar ban nuna kishin addini sosai ba yadda har zan iya sa begen makoma mai kyau kamar yadda kake bege ba. Zan iya bada duk abin da nake da shi domin in sami irin wannan bege da gaba-gadi irin naka.”

Sai bakon nasa ya ce, “Ai addini ba tikiti ko kuwa izinin shiga sama bane.” Addini ba ya taba ba wani salama tsakaninsa da Allah ko kuma ya ba shi izinin zuwa gaban Allah ba. Jinin Yesu Kristi kadai ne ke iya bada wannan damar zuwa gaban Allah.”

Sai mara lafiyar nan ya nuna mamakin jin wannan zance. Domin ya saba tunani cewa addini shine ya fi kome a duniyan nan. Kuma duk lokacin da mutane suke maganar “tuba” da “ceto” da kuma “tsarkakewa cikin jinin Kristi” suna bayani ne kawai bisa ga tunaninsu, kuma bisa ga irin tasu bangaskiyar daidai da abin da shi ya dauka cewa shine “addini.” Abokinsa ya lura da wahalar da yake ciki maganar Allah? Mara lafiyar ya nuna amincewa da murna. Daga nan sai ya karanta:

“Ubangiji ya ce wa Musa da Haruna a cikin kasar Masar … A fada wa dukan taron Israilawa … kowanne namiji ya dauki dan rago … da … Zasu yanka … Sa'annan ku debi jinin ku sa a dogaran kofa duka biyu da bisa kan kofar gidajen da za a ci naman dabbobin … A daren, zan ratsa kasar Masar, in bugi kowane dan fari na kasar na mutum da na dabba. Zan hukunta gumakan Masar duka, gama ni ne Ubangiji. Jinin da ke bisa gidajen ku zai nuna inda kuke. Sa'adda na ga jinin zan tsallake ku, ba kuma wani bala'in da zai same ku, ya hallaka ku, a lokacin da zan bugi kasar Masar” (Fitowa 12:1,2,6,12,13).

Ya yi dan bayani kadan akan ayoyin, ya ce “Jinin da aka zubar kuma aka yafa a bisa kofa, aka dogara gare shi, shi kadai, shine ya tsiradda dukan wadanda ke cikin gida a wannan daren.

Dukkan wadanda suke karkashin kariyar jinin sun sami tsira dukkan wadanda ba karashin kariyar jinin ba, kome kyawun halinsu, sun fada cikin hukunci.”

Sai mara lafiyar nan ya tashi zaune ya mika hannu ya kama hannun bakon nasa, a hankali, tare da nuna fahimta, ya ce, “Ashe, duk yana cikin jinin. Yanzu ina iya gani sosai cewa tikiti na samun ceto jinin Kristi ne kadai.”

Akwai mutane da yawa wadanda suke zaton addini za ya cece su. Mutane da yawa suna dogara ga adalcinsu da ayyuka masu zuwa sama. Allah ya fada cewa jini mai tsarki na Yesu Kristi (Wanda masu zunubi ke dogara da shi) shine kadai mafakar hukumci mai zuwa.

“Jinin Yesu Dansa yana tsarkake mu daga dukkan zunubi” (1 Yohanna 1:7).

“In ba gama da jini ba kuwa ba gafara” (Ibramiyawa 9:22).



Free tracts and biblical counsel available by request. Write:
**Word Of Truth,** P.O. Box 1126, Kaduna, Nigeria.